# Littafi mai Tsarki na yara

Ke gabatar da



# Mazan Da Ba Za Su Sunkuya Ba

Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Jonathan Hay
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: Mary-Anne S.

Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org

©2023 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan
har ba zaku sayar da shi.

Sarki Nebukadnezar ya gina wani kato gunkin zinariya. Ya yi shi da zinariya, daga kai zuwa tafin kafa. Watakila sarki ya manta da mafarkin da Allah ya aika a fada masa cewa mulkinsa na zinariya ba zai dawwama ba. Watakila yana gani kamar idan ya gina gunkin da zinariya Kalmar Allah ba zai zama gaskiya ba.



**Daya daga cikin ‘yan hidimar sarki ya karanta dokar ga mutane: “… za ku sunkuya har kasa ku yi sujada ga gunkin zzinariya … Kuma duk wanda ya ki ya sunkuya har kasa ya yi sujada za a jefar da shi a tsakiyar wuta mai tsananin kunna.”**



Kowa ya yi abin da sarki ya umarta – ban da maza uku. Wadannan mazan Ibriniyawa ne. Su ne Shadrak, Meshak, da Abednego, abokan Daniyel. Kamar Daniyel ba ya wurin a lokacin, gama tabas, da shi ma ya ki ya yi sujada ga abin da mutum ya gyara.



**Maza masu hikima na sarki sun yi kishin Daniyel da abokansa saboda sarki ya so su. Sai suka ce, “Akwai maza uku wadanda ka sa suna mulki a kan wadnsu yankuna a Babila – Shedrak, Meshak, da Abednego. Wadannan mazan, ya sarki, sun ki su yi biyayya. Ba sahigima ga allolin ka kuma ba sa sujada ga gunkin zinariya wanda ka kafa.”**





Sarki Nebukadnezar ya cika da fushi. Ya ja musu kunne, “Idan ba ku yi sujada ba, za a jefa ku a cikin wuta mai tsananin kunna. Wane Allah ne zai kubutar da ku daga hannuna?”

Sarki yana yin babban kuskure.  Yana gwada Allah mai rai.  Maza uku na Ibriniyawan nan sun sani ba daidai ba ne ga dokan Allah su bauta wa wani gunki ba.  Sun tsaya cik.  Saboda sun amince da Allah, ba su ji tsoron sarki ba.



**Wadannan maza uku masu karfin hali suna da amsa ga sarki. Suka ce, "Allahnmu wanda muke masa bauta zai iya cece mu daga cikin wuta mai konawa. Amma in ba haka ba, bri ka sani, ya sarki, cewa ba za mu taba bauta wa allolinka ko mu yi sujada ga gunkin zinariya wanda ka kafa ba."**



Sarki Nebukadnezar ya yi fushi! Sai ya ba da umurni a kara zafin wutan har sau bakwai fiye da yadda an saba kunne shi. Duk da haka mazan sun ki su durkusa.



Sai sarki ya umarta mazansa masu ikoa sojojinsa su daura su Shadrak, Meshak, da Abednego,
si jefar da su
a cikin
wuta mai

zafin
konawa.



Gidan wutan ya yi zafi sosai har ma mazan da suka jefar da Shadrak, Meshak, da Abednego su ma zafin wutan ya kashe su.



**Sarki yana dubawa daga nesa. Ya ga yadda a ka jefa maza uku a cikin tsakiyar gidan wuta mai kuna. Amma duka abin da ya gani ba.**



Sarki Nebukadnezar ya yi mamaki!
"Ba mutane uku muka daura muka jefar a wutan ba?" ya tamabaye masu taimakonsa.
"I'i," suka amsa. Ya ce, "Duba! Ina ganin mutane hudu suna a kunce, suna tafiya a tsakiyar wutan, kuma babu abin da ya same su. Na hudun ya yi kamar San Allah!"



Yana matsawa kusa da kofar gidan wuta mai konawa, sarki ya yi ihu, “Shadrak, Meshak, da Abednegor, ‘yan hidimar Allah Mafi Girma, ku fito!” Sai Shedrak, da Meshak, da Abednego, suka fito waje daga gidan wuta mai konawa.



Kowa ya zo ya kewaye su don su bincika Ibriniyawa ukun nan. Sun gani cewa wutan bai sami iko ya konne su ba. Summan kansu bai konne ba ko kadan. Rigunansu ma babu wutan da ya kone. Ko warin wuta ma babu a jikinsu.



**Sa'ad da ya gane abin da ya faru, Sarki Nebukadnazar ya yi wani abu na hikima.  Ya yi addu'a, ya ce, "Albarka ga Allah na Shadrak, Meshak, da Abednego, wanda ya aiko da Mala'ikansa ya kuma kubutar da 'Yan hidimarsa wadanda suka amince da Shi."**



# Mazan Da Ba Za Su Sunkuya Ba

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Daniyel 3

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130


KARSHE

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin
Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake
kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na
kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha
wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya
koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran
zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan
ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka
mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga
cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon
rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka
taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da
zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da
Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16